# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Aljannar Kare – Haɗarin afkawa cikin bashi
## Kashi na shida: Haɗarin gudanar da harkokin bashi

Wanda ya rubuta: James Muhando
Wanda ya fassara: Danlami Bala Gwammaja
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**'Yan Wasa:**

Mai ba da labari: ɗan shekara 30
Ali: ɗan shekara 15
Jamila: 'yar shekara 15
Bash: ɗan shekara 15
Kawu Natanko: ɗan shekara 45
Jami'i mai kula da kwastomomi: ɗan shekara 25
Malam Audu: ɗan shekara 40
Binta: 'yar shekara 11
Iyabo: 'yar shekara 45
Lawan: ɗan shekara 45
Yaron kanti

**Mai ba da labari:**

Masu saurarenmu, barkanmu da sake saduwa a cikin kashi na huɗu na shirinmu na "Ji Ka Karu" mai suna "Aljannar kare – Haɗarin afkawa cikin bashi" wanda wasa ne a kan illar cin bashi. Idan ba ku manta ba sunana Aliyu Bello, jami'i mai kula da bayar da bashi a wannan banki, kuma ni ne zan jagoranci wannan wasa.

Idan ba ku manta ba a kashin da ya gabata na ba ku labarin yadda mahaifiyar abokina Bash ta ladabtar da shi saboda ya yi mata ƙarya cewa yana zuwa makaranta. Bayan haka ne sai muka haɗu a bakin kogi ni da Jamila da kuma Bash inda muka zauna muka tattauna matsalar da Bash yake fuskanta ta keken da ya karɓo bashi. To, ni a tawa gurguwar dabarar, sai nake ganin za mu iya cin bashi a gurin wani mai bayar da bashi da ruwa a ƙauyenmu mai suna Malam Ado. Sai dai kuma dole sai an ba shi wata kadara wadda zai iya riƙewa idan har mun kasa biyansa kuɗinsa. Daga nan kuma wata gurguwar dabara ta sake faɗo min.

**Fitowa ta 1: A gidan su Ali**

**Ali:** Shh! Ya kamata mu dinga kula. Mu tafi a hankali! Kuma mu dinga magana a ƙasa-ƙasa!

**Jamila:** Amma ai har yanzu ba ka gaya mana abin da muka zo yi a nan gidanku ba! Wai laɓe-laɓen me muke ta yi ne haka?

**Ali:** Na ce miku ku ɗan yi haƙuri mana ku gani ! Za mu ɗauki rikodar Kawu Natanko ne mu kai wa Malam Ado a matsayin kada...

**Bash:** A matsayin kadara mana!

**Jamila:** A matsayin me? Kai! Ban gane ba. Wai kuna nufin mu saci rediyon kawunka, mu jinginar da ita don karɓo bashi daga wajen wannan mutumin**?**

**Ali:** Shh! Ki yi ƙasa-ƙasa da muryarki! Kuma ki sani cewa, Jamila, ɗauka za mu yi ba sata ba!

**Jamila:** Ba cinya ba ƙafar baya! To yanzu me za ka gaya wa babarka?

**Ali:** Kwantar da hankalinki! Ai ba za ta sani ba. Bayan ma rediyon ta daɗe a ɗakina ba a amfani da ita! Kuma kawuna ya kai shekaru biyu bai zo gidan nan ba! Mu dai muna so mu samo rance ne kawai daga wannan azzalumin mai ba da bashin nan. Daga baya idan muka biya shi sai mu dawo da ita cikin ɗakina kafin kowa ma ya san ba ta nan! …
Yauwa, ga ta nan a cikin kwali a saman kwabat! Bash, zo ka dafe mini na ɗauko ta! ... Yauwa! ... Bari mu cire rediyon daga ciki kwali, mu mayar da shi ko da wani zai zo ya duba. … Yauwa! … Ku zo mu fita daga nan! Ku zo mu fita !

**Mai ba da labari:**
Duk sai muka ji daɗi ya kashe mu. A ganinmu mu masu hikima ne. Ashe ba mu sani ba cewa akwai wadda ta fi mu dabara. Wannan kuwa ita ce ƙanwata Binta! Domin kuwa tana ji, tana ganin duk abin da muka yi saboda tana ɓoye a ƙarƙashin gadona kamar yadda ta saba. Yanzu haka ga Kawu Natanko can a cikin gari ya nufi wani banki.

**Fitowa ta 2: A banki**

**Kawu Natanko:** Barka da aiki!

**Jami'i mai kula da kwastomomi:** Yauwa, Yallaɓai, me kake buƙata?

**Kawu Natanko:** Na zo wajen Malam Audu ne!

**Jami'i mai kula da kwastomomi:** To ɗan saurara kaɗan!

**Kawu Natanko:** To, da kyau.

**Jami'i mai kula da kwastomomi:** Halo, Malam Audu. … E, wani ne ya zo wajenka. *Ok Sir.* … Yallaɓai, yaya sunanka?

**Kawu Natanko:** Natanko Bello!

**Jami'i mai kula da kwastomomi:** Yallaɓai, ya ce sunansa Natanko Bello. … To, shi ke nan, *Sir.* … Yallaɓai, bi ta wannan ƙofar, sai ka yi hagu, za ka haɗu da shi.

**Kawu Natanko:** To shi ke nan, na gode.

**Malam Audu:** A'a'a, wata sabon gani! Natanko Bello ke nan! Kana lafiya?

**Kawu Natanko:** Malam Audu, lafiya dai za a ce.

**Malam Audu:** Kai kai kai! Ai kuwa mun daɗe ba mu sadu ba. Ka san fa ba ma rabuwa a lokacin muna makaranta!

**Kawu Natanko:** Wannan ai kafin ka tafi ƙasashen Turai ne. Daga baya ai mantawa ka yi da ni!

**Malam Audu:** Hahaha! Haba, yaushe zan taɓa mantawa da kai! Ka taɓa gaya min cewa kai harkar fulotai kake yi yanzu, ko ba haka ba?

**Kawu Natanko:** Kwarai, haka ne. Wannan ma shi ne dalilin da ya sa na zo wajenka. Kuɗi nake buƙata. Wani aiki nake yi, amma ya tsaya cik saboda rashin kuɗi.

**Malam Audu:** Wato dai yanzu ka zo karɓar bashin banki ke nan ko?

**Kawu Natanko:** Kwarai, ko bashin banki ko kuma dai bashi daga wajen aboki, duk ɗaya ne!

**Malam Audu:** To bari na gabatar da kai a wajen manaja.

**Kawu Natanko:** Tsaya tukuna mu yi da wajewa. Ni fa ba ni da wata kadara.

**Malam Audu:** To, na ji. Kamar nawa kake buƙata?

**Kawu Natanko:** To, ko da dai Dala 1000, ko Dala 400, ko ma dai nawa ne da za su ishe ni na ci gaba da aiki har zuwa lokacin da zan samu kaina!

**Malam Audu:** To, yaushe za ka biya?

**Kawu Natanko:** Nan da wata ɗaya.

**Malam Audu:** To, tun da haka ne, bari na ranta maka a cikin kuɗina amma da sharaɗin cewa za ka biya ni lokacin da ka yi alƙawari. Amma abin da zan iya ranta maka, Dala 400 kacal.

**Kawu Natanko:** Ai kuwa na gode. Wallahi ka tsamo ni daga ruwa, kuma in Allah Ya yarda ba zan ba ka kunya ba.

**Malam Audu:** Ba damuwa.

**Mai ba da labari:**
Allah Sarki, Malam Audu! Bai san dawan garin ba, ga shi an burma shi. Ai daga wannan ranar bai sake ganin ƙeyar kawu Natanko ba har lokaci mai tsawo!
Yanzu bari na koma da ku kan labarinmu. Ran nan ina dawowa gida bayan na samo rancen kuɗin da muke nema daga wajen Malam Ado, amma fa sai da na bayar da rediyon Kawu Natanko a matsayin kadarar lamuni. A lokacin dai jina nake cikin farin ciki saboda na taimaki abokina Bash. Sai dai kuma ban zaci abin da zan taras a cikin ɗakina ba.

**Fitowa ta 3: A gidan su Ali**

| | |
|---|---|
| **Binta:** | Wuuuuu! |
| **Ali:** | Wayyo! Amma Binta, kin tsoratar da ni, wallahi! |
| **Binta:** | Hahaha! Wallahi Ali ka burge ni! Ga shi sai shanawa kake yi! |
| **Ali:** | Kin ga Binta, ki fita ki bar min ɗakina! |
| **Binta:** | Duk na ga abin da kuka yi! Kuma bari ka ji na gaya maka! |
| **Ali:** | Zancen me kike yi ne? |
| **Binta:** | Na ga lokacin da kuka zo kai da abokanka kuka sace rediyon Kawu Natanko! |
| **Ali:** | Tsaya ki ji Binta! Don Allah kar ki faɗa wa kowa! Zan yi miki duk abin da kike so! |

**Binta:** Duk abin da nake so?

**Ali:** E, ko mene ne!

**Binta:** Za ka yi min *homework* ɗina?

**Ali:** Zan yi miki!

**Binta:** Kuma za ka yi min shara?

**Ali:** Wannan ba wata matsala ba ce. Ni dai ba na so ki gaya wa kowa.

**Binta:** Kuma za ka yi min wanke-wanke har na mako ɗaya!

**Ali:** Zan yi miki, amma don Allah ban da wanke-wanke!

**Binta:** Mama, wai kin ji abin da Ali...

**Ali:** Na ji, na ji, tsaya, tsaya! Zan yi miki wanke-wanken.

**Binta:** Hahaha! Allah Ya kama ka! Ka ji in gaya maka, Mama ma ba ta nan!

**Mai ba da labari:**
Kwatsam kuma sai wata sabuwar matsala ta kunno kai, a lokacin da baban Bash ya tafi kantin Iyabo, wato kantin da ya saba sayan kayan mota, don ya sayi kaya.

**Fitowa ta 4: A kantin Iyabo**

**Iyabo:** Yahaya!

**Yaron kanti:** Na'am!

**Iyabo:** Duba ka ga ko muna da '*belt'* ɗin boksuwaja?

**Yaron kanti:** Akwai!

**Iyabo:** To ɗauko wa wannan kwastoman guda ɗaya!

**Yaron kanti:** To!

**Lawan:** Madam Iyabo, ina kwana!

**Iyabo:** Malam Lawan ke nan! Lafiya lau! Kwana biyu ka ɓuya. Ka san fa harka ba za ta yi kyau ba idan babban kwastoman mutum ya fara wasan ɓuya!

**Lawan:** Haka ne fa!

**Iyabo:** Yau kuma me kake so?

**Lawan:** Ai, ina buƙatar kaya da yawa don na zuba a kantina da ke gareji. Sai dai yau ban zo da kuɗi ba fa.

**Iyabo:** Amma fa Lawan, ka san ba na bayar da bashi. Ko da yake kai ba ka da matsala wajen biyan bashi, kana biya a kan kari!

**Lawan:** To, idan zancen gaskiya za a yi ma, kin san na daɗe ban karɓi kaya bashi ba.

**Iyabo:** Gaskiya ne, in ban da keken da ka aiko ɗanka ya saya makonni biyu da suka wuce. Ka san wannan bashi ka amsa, ko ba haka ba? Yanzu dai mu bar wannan zancen tun da ka riga ka biya kuɗin! Yau me kake buƙata?

**Lawan:** Me? Tsaya, tsaya! Maganar wane keke kike yi ne? Na ce wane keke?

**Iyabo:** Keken nan BMX da ka turo Bash ya karɓa! Yauwa, ga takardar nan da ka turo min. Da na yi niyyar in jefar da ita tun da ka riga ka biya kuɗin.

**Lawan:** Don Allah tsaya. Wai zancen me kike yi ne, Iyabo? Wace takarda kike magana a kai?

**Iyabo:** Ga ta dai, ga ta.

**Lawan:** Ba ni! ... Iyabo, ki ba wa wanda ya kawo wannan takardar keke mai kyau da kike da shi a kantinki. Zan biya cikon kuɗin ba da daɗewa ba. Sa-hannun Lawan Mamuda. ... Wato Bash ne ya kawo miki takardar nan ko?

**Iyabo:** Ba kai ka rubuta ta ba ke nan?

**Lawan:** Ba ni ba ne. Amma dai wannan yaron nema yake ya zama shaƙiyyi. Bari za mu haɗu da shi!

**Iyabo:** To me ya rage kuma, ai ya riga ya biya kuɗin!

**Lawan:** Babu abin da ya dame ni da ya biya ko bai biya ba! Maganar kawai ita ce yana nema ya zama ɗan damfara! Ke dai bari za mu haɗu wani lokaci.

**Iyabo:** To. Malam Lawan, yaya zancen kayan da za ka siya?

**Lawan:** Zan dawo…

**Mai ba da labari:**
A daidai wannan lokaci, mu kuma muna cikin aji da yamma. Bayan an gama darasin lissafi kowa ya gaji yana hamma. Bash kuma ya dawo makaranta. Muna cikin surutu sai kawai…

**Fitowa ta 5: A aji**

**Lawan:** Bash, kai! Bash, zo nan! Wai yaushe ka zama shaƙiyyin yaro ne haka? Na ce, yaushe ka zama ɗan damfara ne? Zo nan!

**Bash:** Wayyo! Kunnena!

**Lawan:** Wato ka yi min ƙarya ko? Wato ka kwaikwayi sa-hannuna ko?

**Bash:** Don Allah ka yi haƙuri! …

**Mai ba da labari:**
Da dai Bash ya so warware wannan matsala tun kafin ta kai haka da ya yi ta hanyar faɗa wa babansa ko kuma Iyabo gaskiyar lamari. To, a ƙwarewar da na yi a matsayin jami'in mai bayar da bashi, idan har ana binka bashi kuma wata matsala ta sa ba za ka iya biya a kan lokaci ba, to abin da kawai za ka yi shi ne, ka tattauna da waɗanda suke binka bashi. Wasu lokutan sukan ɗaga maka ƙafa ko kuma su ƙara maka wa'adin biya.
To masu sauraren, yanzu bari na koma bakin aikina. Kuna iya shiga yanar

gizonmu a dw.de/lbe idan kuna son ƙarin bayani game da wannan shirin namu. Ko kuma ku tuntuɓe mu a shafinmu na ‘Facebook’. Kar dai ku manta ku lalube mu a shirinmu na gaba don jin ci gaban wannan wasa!